# Idan zaku roƙi Allah to ku roƙe shi Firdausi

Daga Ubadah dan Samit - Allah Ya yarda da shi - cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: «Akwai darajoji ɗari a cikin aljanna, tsakanin kowace daraja kamar tsakanin sama da ƙasa ne, Firdausi it ce mafi ƙololuwarsu (a daraja), kuma daga nanne ƙoramun aljanna suke ɓuɓɓugowa, kuma a samanta ne Al'arshi yake. Idan zaku roƙi Allah to ku roƙe shi Firdausi».
[Ingantacce ne] [Al-Tirmithi Ya Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa a cikin aljannar Lahira akwai darajoji da matsayi ɗari, tsakanin kowace daraja a nisa kamar tsakanin sama da ƙasa ne, kuma mafi ɗaukakar waɗanan aljannatan ita ce aljannar Firdausi, daga nan ne ƙoramun aljanna huɗu suke ɓuɓugowa, a saman Firdausi ne al'Arshi yake; idan zaku roƙi Allah to ku roƙe Shi Firdaus; saboda ita ce a saman dukkaninl aljannatan.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee